مكتب الدعـوة والإرشـاد بالمعـذر وأم الحمـام



بااللغة الهوسا

# صفه الوضوء والصلاة

# SIFFAR YADDA AKE YIN SALLAH

# YADDA AKE YIN ALWALA A AIKACE

المكتب التعاوني للدعوة والإرشاد وتوعية الجاليات بالمعذر وأم الحمام



**1**. Idan ka yi nufin yin sallah, farkon abinda zaka fara yi shi ne ka ce "*Allahu Akbar*" ma'ana Alla shi ne yafi girma (fiye da kowa). kuma ka kasance a daidai wannan lokacin ka daidaita a tsaye. Limami zai yi kabbararsa a fili ne domin na bayansa su ji shi, me bin bayan liman kuma zai fada ne a boye sannan mutum zai daga hannayensa ya hade yan yatsunsa yayinda zai yi kabbarar harama har sai ya daidata hannayen nasa da kafadunsa, kuma mamu baza suyi kabbara ba har sai idan liman ya riga ya yi kabbara.



**2**. Sai mutum ya sanya hannunsa na dama akan tafinsa na hagu ko kuma akan tsintsiyar hannunsa na hagu ya damke shi sai ya sanya su akan kirjinsa. ya kuma sanya ganinsa a wurin da zai yi sujada, sannan ya fara da daya daga cikin adduo"in da aka rawaito a sunnar annabi (S.A.W) misali "*Subhanakal lahumma wa bi hamdika wa tabarakas muka, wa ta'ala jadduka, wa la'ilaha gairuka*" sannan ya nemi tsarin Allah daga shedan (isti'aza), ya kuma yi bisimillah, -amma duk wadannan za ayi su ne a boye-, sannan sai karanta Fatiha, amma mabiyin liman ba sai ya karanta komai ba idan dai liman yana karatu a fili. Sai dai an so ya karanta fatiha a lokacin da liman yayi shiru, sannan kuma sai a karanta abin da ya samu na alkur'ani. Liman zai bayyana karatu a sallar Asuba da raka'a biyu na sallar magariba da isha, ragowar sallolin kuma duk a zuci ake yi.

**A kula sosai:** an so mutum ya karanta alkur'ani kamar yadda yake a jere kar ya canja tsarin jerin da alkur'ani ya ke don yin hakan makaruhi ne. kuma haramun ne mutum ya canja jerin kalmomin alkur'anin ko kuma ayoyinsa.



**3**. Sannan sai mutum ya kabbara yayi ruku'u ya kuma daga hannunsa yayin kabbarar, ya kuma sanya hannayensa a kan gwiwoyinsa yayi kamar zai kama su, ya kuma bude yan yatsunsa ya mike bayansa ya sanya kansa a daidai da shi (baya), sannan ya ce " *subhana rabbiyal azim* " sau uku. Idan ka riski ruk'u to ka riski wannan raka'ar.

**A kula sosai:** lokacin da ake cewa "*sami'allahu liman hamidahu* " shi ne yayinda mutum yake dagowa ba sai mutum ya dago ba ko kuma kafin ya dago ba. Inda mutum zai jinkirta fadan da gangan to sallarsa ta baci.



**4**. Sannan sai mutum ya dago daga ruku'u yana mai cewa: "*Sami'allahu liman hamidahu*" kuma ya daga hannunsa, idan ya daidaita a tsaye sai yace: "*Rabbana wa lakal hamdu, Hamdan kasiran dayyiban mubarakan fihi mil'assamawati wa mil'al ardhi wa mil'a ma shi'ta min shai'in ba'adu* "

**A kula sosai:** ba a cewa"*Rabbana wa lakal hamdu*"har sai an tabbatar cewa an daidaita a tsaye.



**5**. Sannan sai mutum ya tafi sujada yana mai yin kabbara, sai mutum ya nesanta tsakanin damatsansa da hakarkarinsa, da kuma tsakanin cikinsa da cinyoyinsa, kuma ya sanya hannayensa daidai da kafadunsa, ya kuma kafe digadigansa ya sanya 'yan yatsun hannayensa da kafafuwansa su kalli alkibla, sannan ya ce: "*Subhana rabbiyal a'ala*" sau uku.

**A kula sosai:** Tilas ne ayi sujada akan gabobi bakwai: geffan digadigai guda biyu, gwiwoyi biyu, tafukan hannu biyu, goshi da hanci; idan mutum ya bar wata gabar bai yi sujada da ita ba da gangan, to sallarsa ta baci, saidai da wani uzuri.



**7**. Idan mutum ya kammala raka'a ta biyu sai ya zauna domin tahiyar farko,yana mai shimfida kafarsa, ya sanya kafarsa ta hagu akan cinyarsa ta hagu, ya sanya hannunsa na dama a akan cinyarsa ta dama ya kuma damke dan karamin yatsansa da mabiyinsa, ya kuma yi kawanya a tsakanin babban dan yatsansa (ibham) da kuma dan yatsansa na tsakiya (wusda) sai kuma yayi nuni da manunin dan yatsansa (sabbaba) sai yace: *"At tahiyatu lillah, was salawatu waddayyibatu, assalamu alaika ayyuhan nabiyyu wa rahmatullahi wa barakatuh, assalamu alaina wa ala ibadillahis salihina, assh'hadu an la'ilaha illallahu, wa assh'hadu anna Muhammadan abduhu wa rasuluh"* sannan sai ya mike domin raka'a ta uku da ta hudu idan sallar me hudu ce, ko me uku. Yana me kabbara tare da daga hannu, haka dai har ya idda sallar. Sai dai ba zai bayyana karatunsa ba, kuma fatiha kawai zai karanta.




**8**. Sannan sai ya zauna domin tahiya ta karshe ( a sallah me raka'a uku ko hudu) zai zauna akan duwainiyarsa, shima zaman ya kasu daban-daban dukkaninsu sun inganta. 1) mutum zai shimfida kafar hagu ya kuma fito da ita ta bangaren dama ta karkashin kwaurinsa, ya kuma kafe kafarsa ta dama da duwainiyarsa akan kasa. 2) ko kuma ya shimfida kafar hagun ya fito da ita ta dama tsakanin kwaurinsa da cinyarsa da duwainiyarsa akan kasa, ba zai zauna bisa duwainiyarsa ba sai a tahiyar karshe a sallar da take da sama da tahiya daya, sannan sai ya ce: *at tahiyatu lillahi…"* sannan yace: *" Allahumma salli ala Muhammadin wa ala ali Muhammadin kama sallaita ala Ibrahima wa ala ali Ibrahima innaka hamidun majid, Allahumma barik ala Muhammad wa ala ali Muhammadin kama barakta ala Ibrahima wa ala ali Ibrahima innaka hamidun majid ".*

**kuma ana so yayi addu'a bayan tahiyar kamar yadda yazo a sunna kamar:** *" A'uzu billahi min azabin nari, wa azabil kabri, wa fitnatil mahya wal mamati, wa fitnatil masihid dajjali ".*



6. Sannan sai mutum ya dago daga sujada tare da kabbara ya kuma zauna. Shi kuma zaman iri biyu ne: 1) ko dai mutum ya shimfida kafarsa ta hagu ya kuma zauna a kanta, sannan ya kafe kafarsa ta dama ya sanya 'yan yatsunsa su kalli alkibla. 2) ko kuma mutum ya kafe digadigansa da 'yan yatsunsa duka su kalli alkibla ya kuma zauna a kan mazaunansa. Kuma ya ce "*Rabbig firli*" sau uku, za a iya karawa da "*Warhamni wajburni, warzukni, wansurni, wahdini, wa afini, wa'fu anni*"itama sujada ta biyu kamar yadda akayi ta farko sannan sai a dago daga sujada tare da kabbara. Sai kuma ya zabura ya mike tsaye da digadigansa, ya kuma raka'a ta biyu kamar ta farko.

**A kula sosai:** Ba a karanta fatiha har sai an tsaya tukuna, idan aka fara karanta ta kafin a mike to tilas ne a sake karanta ta bayan an mike, idan kuma ba haka ba to sallah ta baci.



9. Sai kuma mutum yayi sallama, ya juya bangaren damansa ya fadi " "*Assalamu alaikum wa rahmatullah* " Sannan yayi a bangaren hagunsa. Idan kuma yayi sallama to sai kuma yayi addo"in da suka zo a sunna, yana daga zaune awurin da yayi sallah.





Salla bata yiyuwa saida alwala kuma tilas alwalar ta zamanto anyi ta da ruwa mai tsarki wanda shine: ruwan da bai canja daga asalin kamanninsa na ruwa ba, kamar ruwan kogi ko na rijiya ko na idaniyar ruwa ko na korama.

**A kula da kyau:** komai kankantar najasa takan lalata ruwan da yake dan kadan, ma idan yana da yawa kamar ya haura lita (210) to najasa bata lalata shi har sai idan ta canja masa kala ko dandano ko kuma kamshi.



**1.** Ana fara alwala da sunan Allah (bisimillah) kuma an so a fara da wanke tafukan hannu a kuma tabbatar sun fita, za ayi hakan sau uku, musamman ga wanda ya farka daga barci

**A kula da kyau:** Ba a son a wanke wata gaba sama da sau uku wannan "MAKARUHI" ne.



**2.** Sannan sai kurkurar baki, tilas ne ayi kurkura na farko, amma idan aka yi sau uku to shi yafi soyuwa kuma yafi falala.

**A kula da kyau:** zuba ruwa a baki da fitar da shi kadai baya wadatarwa, dole ne sai an kurkura shi a cikin bakin. Kuma an so mutum yayi asuwaki yayin kurkurar bakin.



**3**. Sannan sai shaka ruwa a hanci, tilas ne ayi sau daya a kalla, amma idan anyi sau uku shi yafi falala.
**A kula da kyau:** itama shakar hanci ba wai kawai za a shigar da ruwa hanci ba ne, dole ne ya zamo ta hanyar shakar ruwa tare da numfashi, kuma ya shiga har cikin hancin sannan a fyato shi ya fito tare da numfashi.



**4**. Sannan sai wanke fuska, itama tilas ne ayi sau daya a kalla, amma idan anyi sau uku shi yafi. Za a wanke ta ne tun daga kunnen dama zuwa na hagu, wannan a kwance kenan, a tsaye kuma tun daga karshe haba har ya zuwa mabubbugar gashin kai.
**A kula da kyau:** Idan gemun mutum yana da yawa to an so ya tsefe shi, amma idan bashi da yawa to tilas ne ya tsefe shi ta yadda ruwa zai ratsa hi.



**5**. Sannan sai wanke hannaye tun daga yan yatsu har zuwa guiwar hannu, tilas ayi na farko amma idan an kara zuwa uku wannan shi yafi.
**A kula:**Ana so a fara da hannun dama kafin ayi na hagu,da kuma cuccuda su.



**6**. Sannan sai shafar kai baki dayansa, mutum zai shigar da yan yatsunsa guda biyu manuniya (sabbaba) cikin kofofin kunnuwansa, sannan ya shafi fatun kunnuwansa da manyan yan yatsun nasa (ibhama).

**A kula da kyau:** inda ya wajaba a shafa a kai shi ne: daga mafarin fuska zuwa keya. Kuma idan gashi yana da yawa ba lalle ne sai an shafi wanda ya sauko ba. Idan kuma babu gashin kwata- kwata to sai a shafi fatar kai kuma tilas ne a shafi fatun kunnuwa.



**7**. Sannan sai mutum ya wanke kafafuwansa shima sau daya ne ya wajaba, amma idan aka yi sau uku ya fi falala.

**FADAKARWA: 1.**.Wuraren da ake wankewa a yayin alwala guda hudu ne;**(a)** kurkurar baki da shaka ruwa da wanke fuska **(b)** hannaye **(c)** shafar kai da kunnuwa **(d)** kafafuwa zuwa idan sawu. **2.** Tilas ne a wanke wadannan gabbai a jere daya-bayan -daya, idan kuwa aka bar wata gabar ba a wanke ta ba har jiki ya bushe, to alwala ta baci.

**3.** An so mutum idan ya kammala alwalar ya ce: " **ASH-HADU ANLAIILA'HA ILLALLA'HU WA ANNA MUĤAMMADAN ĂBĐUHU WA RASULU** " "Na shida babu abin bauta bisa cancanta sai Allah shi kadai yake bashi da abokin tarayya, kuma na shaida annabi muhammadu bawan Allah ne kuma manzonSa ne.


موقع المكتب على
خرائط Google

الحساب العام
SA 21 8000 0251 6080 1007 5881
حساب الوقف
SA13 8000 0251 6080 1017 7778

+966 11 488 4496
+966 11 482 7489
+966 55 0886 610
info@yaqeenweb.com
yaqeenweb
www.yaqeenweb.com